Darasi na 1

# Farkon Tafiya



## A Duba a Takaice

Manufa

Dalibai za su:

- gane cewa suna girma zuwa zama manya kuma L.M.T. zai yi musu jagora, ya gargade su kuma ya kare su daga hatsari;
- yi kaunar sauraro da bin shawarar da Allah ya bayar a Maganarsa;
- sami karfafawa ayayi da muke sani cewa Yesu ba ya sakewa.

**Daga Maganar Allah**

Karin Magana 1:7-10, 29-33
Luka 2:52
1 Timoti 4:12
Romawa 8:28, 31, 34-39
Ibraniyawa 13:8

**Abin da kake Bukata**

- domin Ayyuka, doguwar takarda ko kyalle don gyara tuta;
- fensura masu launi ko maka.

**Haddacewa:**
Karin Magana 1:7

## Farawa

Fadi wannan labari —ka dauka cewa, kana tuka mota a kan gangara. Ba ka taba bin hanyar ba, bakuwar hanya ce gare ka. Sai kawai ka ga rubutu cewa: *" Birnin Manya. Shekaru takwas nan gaba."* Ka ci gaba da tuki, kana marmarin isa birnin da ka ji labarinsa. Kana cikin tafiya bayan ka sha kwana sai ka ga wani mutum yana daga jar tuta. Ya ba ka alama don ka tsaya, sai ka taka birki. Sai ya ce, "Ina tsaye a nan don in ba ka muhimman bayani. Akwai gada a gaba wajen kilometa daya daga nan kuma tana da babban rami. Idan ba ka yi hankali ba za ka fada ciki. Bayan haka ba za ka isa Birnin Manya ba." *Me za ka yi?* Babu wata motar da ta iso nan da ta koma da baya. Da ka tambayi mai tutan nan abin da za ka yi sai ya ce, "Ka ci gaba da tuki a hankali a wannan hanya. Idan ka isa inda gada ta baci, sai ka bi hannun dama, ka yi tafiya na tsawon kilometa daya. Daga nan za ka sake samun hanya, sai ka ci gaba da tafiyarka, ba za ka fada rami ba."

TATTAUNA ma'anan wannan labari. Motar da kana tukawa tana zaman ranka. Mai tutan nan da ya tsaya a gefen hanya shi ne littafin darasin nan. Wadannan darusa an rubuta su ne domin KA, karamin matashin da ke kan hanya zuwa babban mutum. Idan ka saurara kuma ka koya daga darusan nan, Allah zai more su ya jagorance ka. Ta haka za ka kare kanka daga faduwa ko lalacewa ko mutuwa a ramummukan da ke kan hanya zuwa zama babban mutum.

FADA—Yau za mu dubi wasu ayoyi don mu san abin da L.M.T. ya fada a kan tafiyan nan da muna ciki.

## Gano Gaskiya

### Rukuni na 1

Dubi ayoyi na biye. Dubi wadansu ka'idodin da za su taimaki kananan matasa su tsaya a kan hanya mai kyau. Karin Magana 1:7-10, 29-33. *Ta yaya za mu fara inganta hikima da sani a rayuwa (aya 7)?* (Ji tsoron Allah. Jin tsoron Allah yana nufi a yi rayuwar da za ta gamshe shi, kuma a san yana nan a kowane lokaci.) *Matashi mai hikima zai saurari wanene (aya 8)?* (Iyaye ko wasu manya masu hikima.) *An gargade mu kada mu saurari su wanene (aya 10)?* (Masu zunubi, wadanda ba sa tsoron Allah.) *Me zai faru da wanda ba ya jin shawara ko tsoron Allah (aya 29-32)?* (Za su sa kansu cikin hatsari.) *Me zai faru da mai jin shawara (aya 33)?* (Za su zama masu albarka kuma Allah zai kare su.)

* **Luka 2:52.** *Ta wadanne hanyoyi hudu ne Yesu ya yi girma a lokacin shekarunsa na karamin matashi?* (Hikima—tunani, girma jiki, tagomashi gurin Allah—ruhaniya, tagomashi wurin mutane —na zaman jama'a.) Yesu ya yi rayuwar dan matashi kuma ya san yadda ka ke ji!
* **1 Timoti 4:12.** *Bulus yana Magana da Timoti wanda yake matashi. A kan wadanne fannoni ne ya fada wa Timoti da ya zama gurbi? (Magana, rayuwa, kauna, bangaskiya da tsarki.) A tunaninka, don me Bulus ya ambaci wadannan bangarori musamman?*
* **Romawa 8:28, 31, 34-39.** *Cikin wadannan ayoyi wace za ta karfafaka a tafiyar nan zuwa girma?* (Akwai amsoshi da yawa. Bari dalibai su fadi ra'ayoyinsu.)

### Rukuni na 2

Daliban su rabu cikin kungiyoyi don su cika **Shafin Dan Matashi.**

## Kalubala

KARANTA "**Kwayar Magana**" a **Shafi Dan Matashi** tare. TUNA wa daliban cewa darusan da ke wannan littafi za su taimake su shiryawa domin wannan lokaci na babban canji saboda kada su fada munanan ramuka masu hatsari na gaba. Ka ba su shawara su rika sauraron shawarar Allah daga Maganarsa ta wurin karantawa a kadaice tare da rokon Allah ya taimake su.

## Ayyuka

FADA—Akwai mutum daya da ba ya sakewa a dukan abubuwan da ke sakewa: SHI NE YESU! (Dubi Ibraniyawa 13:8) Rubuta kalmomin nan a kan babbar takarda sai ka sa launi. YESU—ABOKIN DA BA YA SAKEWA A TSAKIYAR ABUBUWA MASU SAKEWA.

Darasi na 1

# Farkon Tafiya



Kowace aya a nan tana fada mana cewa rayuwarmu na Kirista tana kama da tafiya ko tsere. Ka hada ayar da ta zo daidai da maganar da ta dace.




**Karin Magana 1:7**

In kana so ilimi dole ne ka fara da tsoron Ubangiji. Jahilai ba su san darajar hikima ba, sun kuwa ki su koya.

1. 1 Timoti 4:7-8
2. 1 Korantiyawa 9:24-25
3. Ibraniyawa 12:1-2
4. Ayyukan Manzanni 20:24

A. Karasa tafiyar da kyau ya hada da shaida wa mutanen da ke kewaye da mu Bishara.

B. Allah zai ba da lada ga wadanda suka gama tafiyarsu da kyau.

C. Zuba ido ga Yesu, wanda ya gama tafiyarsa da kyau, zai taimake mu mu gama tserenmu da kyau.

D. Dagewa a tsere zai taimake ka samun lada. Yin kwazon da Kirista zai yi shi ne ya faranta wa Yesu rai.

## Kwayar Magana

Shekara na zama matashi shi ne babban lokaci na sakewan da za ka taba yi a rayuwa. Ba laifi ba ne idan ka ji ba ka gane kanka a wannan lokaci ba. Don ka kare kanka, ka saurari shawara daga iyayenka da manya Kirista masu tsoron Allah. Fiye da wannan duka sai ka saurari shawarar Allah daga Maganarsa! Ka karanta Maganar Allah tare da yin addu'a a kowace rana. Tuna cewa idan kai dan Allah ne, alkwarinsa ba zai taba sakewa ba, kuma zai kasance tare da kai kowane lokaci.